


# Kura a Gandun Dabbobi

Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 4

Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:

Kafin a fara amfani da wannan tsarin koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: • San amon sautukan haruffan Hausa; • Iya gane kalmomin da aka saba da su.

Kura a Gandun Dabbobi
Hausa Nigeria


Copyright © 2017, Enabling Writers Project - American University of Nigeria


http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye hakkin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN
Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor
Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants
Nas Yakubu Bloom Trainer
Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi
Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright:  SIL International 2009




A gandu akwai dabbobi manya da ƙanana. Akwai zaki da kura da giwa da damisa. Akwai jaki da doki da raƙumi. Kuma akwai ɓauna da barewa.

A gandun kuma akwai ɗawisu da akuya. Akwai kaza da shanu da ɓera da kyanwa. Dabbobin duk suna zama lafiya. Ba su faɗa da junansu.

















Zomo yakan yi wasa da zaki. Ɓera ma yakan yi wasa da kyanwa. Dabbobi ba su farautar juna.










Kare da raƙumi sukan ci abinci tare. Jaki da ɗawisu suna wasa tare. Kaza da shaho suna ziyarar junansu. Kowa yana jin daɗin rayuwar gandu.






Wata rana sai kura ta shigo gandu. Kura ta ga dabbobi suna zaman lafiya. Kura ba ta son su zauna lafiya. Sai ta fara kaima dabbobin ziyara gida gida.






Kura ta ba jaki shawara. Ta hana jaki wasa da ɗawisu. Kura ta tafi gidan zomo. Ta hana zomo ziyarar zaki.







Kura ta shiga tsakanin dabbobi. Yanzu ba dabbar da ta yarda da wata. Kura ta samu abin da take so. Tana son ta samu damar cinye ƙananan dabbobi.




Kullum ƙananan dabbobi sai ragewa suke yi. Kura ke kama su tana cinyewa. Kowa ya gaji da ɓacewar ƙananan dabbobi. Dabbobin sun yanke shawarar su taru wuri ɗaya.





Kura ba ta zo wurin taron ba. Tana can tana aikata ɓarna. Ashe zaki ya ga kura a kan hanyarsa. Zaki ya jawo kura zuwa wurin taro.



Zaki ya sa an hukunta kura. Kuma an kori kura daga gandu. Dabbobi suna zaman lafiya yanzu. Dabbobi ba su sake gudun junansu ba.

ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT

USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE

World Vision

Australian Aid

GLOBAL READING NETWORK